## WAKAR LABBAIKI YA MAIMUNATU TA MARIGAYI AMIRUL JAISHI SHEIKH MUHAMMAD NASIRU KABARA

(wakar da Jikan Marigayin Al-fatih Kariballah Al-Kabary yayi Ishara Izuwa Gareta)

Note: Wannan copy da mukayi amfani dashi wajen Tarjama wannan waka daga Ajami zuwa hausar book copy ne da Sheikh Musal Qasiyuni ya taimaka wajen fitar dashi.

1. Labbaiki Ya Labbaiki Ya # Labbaiki Ya Maimuna.

2. Na'a ma Nuna - Na'ama Nuna # Na'amanu Wadin Maimuna.

3. Wadil araki gaya mana # Loton da za muga maimuna.

4. Begenta ya gasa Zuciya # Ya kul-kulan da dun duna.

5. Duka Kulluhum gaba daya # Yabonki ne mu Maimuna.

6. Ranar Alastu Birabbikum # Muka Kulla Sharadi Maimuna.

7. Ranar Alastu Birabbikum # Na Gaida ke Maimunatu.

8. Ranar Alastu Birabbikum # Kin Tara Kowa Munatu.

9. Ranar Alastu Birabbikum # Kin Tambayo ya Maimuna.

10. Kika ce kAlastu Birabbikum' ? # Muka ce 'Bala Ya Maimunatu'.

11. Kikace mu kawo Alkawar # Muka ce na'am ya Maimunatu.

12. Labbaiki Ya - Labbaiki Ya # Labbaiki Ya Maimunatu.

13. Tutar Sama Ranar Bala # Ta Karkatowa Maimunatu.

14. Ranar Bala dukkan rusun # Tashi gaban Maimunatu.

15. Ranar Bala Ush-shaku sun # Narke Gaban Maimunatu.

16. Ranar Bala Aqdabu sun # Sha'ani gaban Maimunatu.

17. Ranar Bala Jilani Yayi # Shagali Gaban Maimunatu.

18. Mahdiyyu ma Ranar Bala # Ya Girgiazawa Munatu.

19. Ranar Bala KHAIRUL WARA ne # Shamakin Maimunatu.

20. Ranar Bala KHAIRUL WARA ne # Du Garin Maimunatu.

21. Sammani Ma Ranar Bala # Yace muzo muga Munatu.

22. Ya Tara Yayan sa don # Suyi gaisuwa Gun Munatu.

23. Sahl Ibn Abdillahi ma # Ya Nuna. Zinar munatu.

24. Na Khadija baimana yayyafi # Da Ruwan Sanin Maimunatu.

25. Mune madoka Tamburan # Daula gaban Maimunatu.

26. Mukhtar baiman Yayyafi # Da ruwan sanin Maimunatu.

27. Wasu tun a can bisa gantaba # Suka Fandarawa Munatu.

28. Mukasha zamam mu cikin haka # Gamu munai ga Munatu.

29. Kuma sai ta sa mana Shamaki # Don Kar mu gane Mu

natu.

30. Kuma sai ta samana Mantuwa # Domin Mance Munatu.

31. Bayan zamani mai tsaho # Sai Gamu ga Maimunatu.

32. Ta Yaye dukkan Shamakiy # a gaban mazajen daibatu.

33. Wato nufi na Annabawa # Jarumanta na Makkatu.

34. Haka na take Kul Safiya # Ta kashe ta raya Munatu.

35. Daular Sanin Rahamaniyya # Da Muhammadiyya Qurbatu.

36. Itace bukatar zuciya # Acikin sarautun Munatu.

37. Wa dil Araki kina ina # Na'ama nu Nuna Munatu.

38. Wa dil Araki dake nake # Na'amanu Wadin Munatu.

39. Na'ama nuna - Na'ama nuna # Na'amanu Wadin Munatu.

*Malam Waziri Mai Nasara.*

*09035830253*